Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance Sa’i ɗaya na ruwa yana isarsa a wankan tsarki, kuma musun Nabiy ɗaya yana isarsa a alwala

Daga Safina - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance Sa’i ɗaya na ruwa yana isarsa a wankan tsarki, kuma musun Nabiy ɗaya yana isarsa a alwala.

[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance yana wankan tsarki da sa’i ɗaya, kuma yana alwala da mudun Nabiy ɗaya. Sa'i: Mudun Nabiy haɗu ne, mudun Nabiy kuma: Gwargwadan cikin tafuka biyu na mutum madaidaicin halitta.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/65371